# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Almara a Afirka domin al'adu da zaman lafiya:
## Bari na ba ku labari
## Na biyu: Hikayar Zaki da Kura da Ungulu


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Ibrahima Ndiaye |
| Waɗanda suka tace: | Yann Durand, Stefanie Duckstein, Naïma Guira |
| Wanda ya fassara: | Ɗanlami Bala Gwammaja |


**'Yan wasa:**

Mai ba da labari

Manyan Dawa Zaki

Kura

Ungulu

MAI GABATARWA:

Masu sauraronmu, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin shirinmu na “Ji Ka Karu” inda a wannan karon mun zaɓo muku hikayoyi ne da labarurruka da ke raya al’adu da kuma kawo zaman lafiya, sannan kuma da yin sulhu tsakanin al’umma. Misali, hikayoyin za su koya muku yadda mutane za su warware wata matsala idan ta faru, da yadda za su iya magance cin amana da hassada da kuma son kai. A kowace hikaya da za mu kawo, za ku ji wani abu mai amfani da zai taimaka muku a yanzu ko kuma nan gaba.

A shirin namu na yau, za mu ji yadda aka yi Kura take da ƙashin baya ɗan ƙarami, da kuma yadda Ungulu ya sami sanƙo. Don haka sai ku ba mu aron kunnuwanku domin sauraron “Hikayar Zaki da Kura da Ungulu”.

MAI BA DA LABARI:

Wata rana an wayi gari kamar yadda aka saba, rana kuma ta fito da haskenta, ga kuma iska mai daɗi tana bugowa daga teku. To a wannan rana, bayan Zaki ya gama cin abinci, sai ya yanke shawarar ya kwanta a ƙofar gida ya ɗan sha wannan iska mai daɗi. Bayan da ya yi hamma har sau biyu, sai kawai ya kama barci. Bajewar da ya yi a kan ganyayyaki masu laushi ta sa ya daɗa samin nutsawa sosai a cikin barcin nasa, har ma yana mafarki.

A daidai wannan lokacin da muke magana kuma, kamar an haɗa baki, sai ga Kura ta zo wucewa. Can a kusa da Zaki kuwa, sai ta hango wata barewa da ya ci ya rage, wadda da ma ita ce abincin da ya fi daɗaɗa masa rai. Ba tare da wani ɓata lokaci ba, sai ta lallaɓa a hankali, ta janye wannan barewa ta shige wani lungu nesa da inda Zakin yake. Kwatsam, sai Zaki ya yi hamma wanda hakan ya sa Kura ta tsorata ta sulale.

Wannan ya sa Zaki ya farka, sai ya yi kiran Kura ya ce ta dawo.

ZAKI:

“Au, ashe Kura ke ce ma. Ai bai kamata ki dinga tsorata da ni ba. Na tabbata kina jin yunwa. Zo don Allah, kar ki ji tsoron kome don kin ci

abincina!"

MAI BA DA LABARI:

Sai dai kuma fa, Kura ba ta amince da wannan gayyatar da Zaki ya yi mata ba.

KURA:

"Kai, ni fa ban amince maka ba."

MAI BA DA LABARI:

Sai dai kuma ta faɗi haka ne fa a gigice, domin kuwa bakinta ya bushe sai hangame shi take yi, ga ƙafafuwanta sai nema suke su kasa ɗaukarta, ga kuma idanuwanta duk sun yi zuru-zuru. Ga kuma ƙasusuwan haƙarƙarinta duk sun fito. Cikinta kuwa, sai kiran ciroma yake ta yi. Duk da haka, amma tsoro take ji ta karɓi wannan tayin da Zaki ya yi mata.

ZAKI:

"Ke kuwa don Allah me ya same ki ne? Kin san fa na riga na ƙoshi. Kar fa ki bar garaɓasa ta wuce ki. Kin san fa irin daɗin naman barewa, kuma ban daɗe da kama ta ba. Ni tun da naman ya wadace ni, bai kamata na ci ni kaɗai ba. Kamata ya yi a ce na yi wa wani tayi. Ai, cin abinci da mutane ya fi kome a duniya. Don Allah ki zo ke ma ki ɗan sa albarka, kuma kin ga ma sai mu ɗebe wa juna kewa."

MAI BA DA LABARI:

To kun san Kura da kwaɗayi, nan da nan sai Zaki ya shawo kanta.

ZAKI:

"Ki zauna kawai, ki ci naman nan son ranki."

MAI BA DA LABARI:

Zaki fa ke nan yake gaya wa baƙuwarsa Kura. Zamanta ke da wuya

kuwa, sai Kura ta fara ba da labarin gari, da kuma yadda kowa yake fama, abu dai kamar ba zai ƙare ba. Har cewa take wai tausaya wa waɗanda ke cikin irin wannan matsi na rayuwa take yi, sai dai kuma kowa zai iya gane abin da take faɗi bai kai zuci ba.
To, suna cikin cin namansu cikin jin daɗi, sai ga Ungulu ya kawo kai. Da ma dai ya daɗe yana shawagi yana kallon wannan zama saboda abin ya ba shi sha'awa.

UNGULU:

"Barkanku da himma. Lalle na ga kuna jin daɗin abincin nan. Da ku ɗan rage mini mana. Wallahi, cikina sai ƙugi yake tun safe."

ZAKI:

"Haba, ai wannan ba wani abu ba ne. Bismillah mana, Ungulu. Ai duk naman zai ishe mu mu ukun!"

MAI BA DA LABARI:

Mai masaukin baƙi duk ya gayyaci baƙinsa cikin karamci. Saboda wannan sauƙin kai na Zaki, da kuma barkwancinsa, sai ya sa hirar tasu ta yi armashi, wadda kusan ba su taɓa yin irinta ba.

UNGULU:

"Wallahi na ji daɗin zuwa wajen nan naka, yallaɓai, saboda zaman kaɗaici ya dame ni. To amma ni kaina da na yi wani tunani, sai na gane matsayina cewa ni fa ɗan tsuntsu ne wanda ba shi da kowa. Sam ba na jin daɗin rayuwata. Duk lokacina yakan ƙare a kan bishiya ne, ina wasiwasin wannan zaman banza da nake yi. Wallahi wannan abu yana ban takaici."

KURA:

"Kai ma dai da abin dariya kake. Da zaman kaɗaici yana kisa, ai da tun tuni daga cikin kabarina nake maka wannan maganar."

ZAKI:

“Ni ma dai ra’ayinmu ɗaya da ke Kura, don kuwa da hammar da nakan yi ta zaman kawai na kisa, da tuni an binne ni da bakina a hangame.”

MAI BA DA LABARI:

To kun ji fa ta bakin Zaki, kuma duk sun yi na’am da haka.

ZAKI:

“To idan har duk ra’ayinmu ɗaya, me zai sa mu ukun ba za mu zauna a wuri guda ba, a kogona?”

MAI BA DA LABARI:

Nan da nan sai Kura da Ungulu suka fara ɗoki a kan wannan magana ta Zaki. Sai dai kuma akwai fa wani sharaɗi guda ɗaya wanda dukkansu sun amince da shi, cewa kada wani ya taɓa kayan wani. Su duka sun amince da wannan sharaɗi, don haka nan da nan sai suka tare a cikin kogon Zakin a lokaci guda.
Sai dai kuma fa wannan zamantakewa wadda aka fara ta cikin farin ciki, ba ta ɗore ba. Ba a daɗe ba, wata rana sai Zaki ya kaso wata barewa, wadda ta fi wadda ya taɓa kawowa girma, ya zo da ita gida. Kun ga ke nan nama zai ishi kowa, don haka sai ya yi wa abokan zamansa tayin su zo a yi wannan shagali da su. Da yake garin ya yi sanyi a wannan yammacin, sai ya hura wuta don a ji ɗumi. Don haka kafin ya fara dafa naman, sai ya ɗan kishingiɗa don ya ɗan runtsa. Barci sai ya kwashe Zaki, yana hamma yana minshari, har ma kuma ya fara mafarki mai daɗi yana murmushi. To fa gaskiya wannan barci yana ɗan damun Kura tun da ita cikinta ba kome. Don haka sai ta wawashe naman barewar gaba ɗaya ta gudu ta ɓuya, tana shirin kafa wa naman nan fiƙarta ke nan, sai Zaki ya farka.
Sai Zaki ya mangare ta a baya ta faɗa cikin garwashin wuta. Sai garwashi ya tashi ya watsu ko’ina, har ma wani ya faɗa kan Ungulu. Cikin tsoro sai Ungulu ya yi fuka-fuka da fikafikanshi har ya samu ya

tsere daga kogon Zakin, ita kuma Kura na biye da shi, tana tafiya bayanta a duƙe.
To fa tun daga wannan ranar, Ungulu yake da gwaguyayyen kai. Ita kuwa Kura daga wannan ranar ta fara tafiya da duƙaƙƙen baya. Kuma idan tana tafiya sai a ga kamar tana son ta ɗan sosa zafin ciwon da yake bayanta ne a ƙasa.
Wannan ita ce hikayar tamu ta yau. Duk wanda ya yi amfani da darussan da ke cikinta, to shi kam ya rabauta.

MAI GABATARWA:
Kash! Abin takaici. An yi ƙarkon kifi a wannan hikaya tamu mai taken "Hikayar Zaki da Kura da Ungulu". Masu saurare, mene ne ra'ayinku a kan wannan hikaya? Ko kun taɓa jin cewa kowa ya mallaki kome? Kuma shin ba a taɓa samun wani ya zo don ya ɗebi wani abu ba tare da an ba shi ba? Anya kuwa kuna ganin za a iya rayuwa cikin zaman lafiya ba tare da fuskantar wata matsala ba? Muna jiran ra'ayoyinku a rubuce ta adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe.